# Azumin Watan Ramadhan

---

<"xml encoding="UTF-8?>

**Meyasa aka yi umarni da yin azumi musamman acikin watan Ramadan wa Musulmai?**

Watan Ramadan shine wata na tara a kalandan mai amf ani da wata na Islama. Tun da shekaran irgen juyin wata yana da gibin sati daya d a rabi in an kwatanta shi shekaran irgen juyin rana, watan Ramadana yana zagayawa ta b aya cikin dukan yanayi. Wata ne mai tsarki saboda Allah ya zabeta donsaukar da litt afi mai tsarki. Imam Ja'far as-Sadiq ya nakalto daga Annabin Tsarki, tsira da amincin su tabbata a gare shi da iyalinshi, cewa,

"Littafan Ibrahim an sauko dasu a daren farko na wa tan Ramadana; Attaura an saukar a ranan shida ga watan Ramadan; Injila an saukad da shi a ranan sha uku ga watan . . ., kuma Alkur'ani mai Tsarki ma an saukar das hi a ranan ishirin da uku ga watan Ramadan."

An dauke shi mai tsarki saboda yana da Daren Karfi (Laylatul Qadr) a cikin shi. "Qadr" na nufin makoma a rubuce, kuma a wannan daren Allah ke tsara dukan kowane abu zai auku a cikin shekaran da ke zuwa ga kowani da kuma dukkan halittun shi.

Imam as-Sadiq, aminci ya tabbata a gareshi, ya fada mana cewa,

"A lokacin Laylatul Qadr, malaiku, ruhi, da kuma ma rubutan da aka yadda dasu suna

sauka dukansu zuwa sama na kasa su rubuta duk abun
da Allah ya tsara wannan
shekaran, ikuma in Allah yana so ci gaba da abu ko
ya jinkirta ko ya kara a kai, sai Ya
umurci mala'iku su goge su sa wani sabo a maimakon
duk abun da tsara."
Annabin Tsarki na Musulunci, amincin Allah ya tabba
ta a gare shi da iyalinsa, yayi
mana Magana kan albarkan da ke cikin watan Ramadana
.
"[Watan Ramadana] yana kwarara da falaloli, rahamom
i, a shirye kake ka mika
zunubbanka da ka sani da wanda ba ka sani ba zuwa g
a Allah don ya gafarta maka.
Ranakunshi, da dararrakunshi da awowinshi, a kiyasi
n Allah, sun fi zabi, kyautuwa da
muhimmanci sama da ranakun, da dararrakun da awowin
sauran watannin. Ya kece
sauran watanni a falaloli da ni'imomi ..... Saboda ha
ka, da ikhlasi, ba tare da shaidanci
da tunanin zunubbai da aikatasu ba, tare da kyakkya
wan manufa, kayi sallah ka kuma
roki Allah ya baka zuciya da kwarjinin yin azumi... c
ikin dukan wannan watan.."
Rufewa
:
Musulmai na yin azumi, a yadda suke ko wani irin ai
kin ibada, dan su nemi kusanci da
Allah, su nemi yardan Shi da yafewan Shi, da kuma t
ada ruhin takawa a jikin Dan
Adam. Azumin a wannan watan yana ba wa kalmar Alla
h darajatta da kuma tsarkake
mutum dan shirin daren kaddara da kuma tsammanin ga
far. Azumi hanyan sabunta

taqwa kowani shekara ne, yana bada lada mai yawa a
,wannan watan Rahaman Allah

.wanda shine hanyan Musulunci na mutumin kwarai

An shardanta Azumin a dukan addinan da ke bin
koyarwan Ibrahim
Addinan Yahudu, Nasara da Musulunci duk sun ayyana
yin azumi. Musa ya yi azumi
na kwana arbai'in a Dutsin Sinai a lokacin wahayin
Dokoki Goma. (Exodus 24:18) Duk
da an rage yi yanzu, al'adan Yahudawa ne a yi azumi
lokacin makoki ko kuma a cikin
tsoro. Yawancin Yahudawa da ke aiki da koyar war a
ddini suna azumi a Ranar
Atonement kuma aa sati-daya na juyayin rusa Jerusa
lem a 597 B.C. Isa of Nazareth,
tsarki ya tabbata a gare shi, yayi azumin Ranar Ato
nement da kuma kwana arba'in da
Musa yayi azumi dan ya kauce wa wasiwasin shaidan.
"Sai Ruhi ya ingiza Isa zuwa hamada don Shaidan ya
kwadaitar da shi. Bayan azumin
wuni arba'in da dare arba'in, sai ya ji yunwa."
(Matthew 4:2)
Kristoci da dama suna yin azumin kafun Easter na kw
ana arba'in, ko da yake yanzu ya
kunshi kiyayewa daga wasu daga cikinkayan abinci ne
maimakon dukan abinci da ruwa.
Musulmai suna azumin watan Ramadana kuma suna iya a
zumi a mafi yawn shekaru na
shekara, ba a tilasta ba.
Allah Daya ya umurci azumi wa muminai; kuma tana da

falaloli masu yawan gaske.
Kayan ji dadi na duniya ana iya jimlace su cikin ab
inci da na sha, jima'i, da nishadi.
Azumi yana bukatan kiyayewa daga wadannan ababe, yi
n abu sabanin ababen da jikin
Mutum a tsarin shi yake kiran shi da ya yi don yabi
umurnin Allah.Wannan yana ginawa
da kuma karfafa iya juriyan da mutum ke da shi, ya
kais hi ga kusanci da Mahaliccinshi.
Wasu falalolin azumi sun kunshi:
Azumi yana koyar sa hakuri, ya koyar da juriya da y
in da'a.
Azumi yana kara jin kai ga marasa galihu.
Azumi na gina dagewa a aikin gyara ruhi da kuma rus
he damuwa da son duniya.
Azumi yana da amfani da dama ga lafiyar jiki.
Azumi na iya zaman dalilin samun rabauta daga zunub
i da kuma samun lada mai yawa.
Azumi na daga cikin tsari mai kwari na gyara ruhi d
a jiki.
Azumi na juyayin lokuta masu muhimmanci na addini
.
Azumin Musulmai na watan Ramadan chigaban dogon tar
ihin azumi na masu bin
addinan da suke bin koyarwar Ibrahim. Karuwan da a
ke yi na gyaran kawuka in anyi
azumi ya maida shi hanya mai muhimmanci wajen kara
imanin mutum da kuma aiki da
koyarwan addini.
"Da maza masu azumi da mata masu azumi...Allah ya shi
rya
masu gafara da lada mai yawa."
(( Alkur'ani 33:35

Me azumin watan Ramadan ya kunsa?
A takaice, azumi ya kunshi gujewa daga dukan abinci
, shaye-shaye, maganan banza, da
jima'i ga ma'aurata daga kafun ketowan alfijir loka
cin da sama yayi haske za a iya
bambanta bakin zare daga farin zaren horizon, har z
uwa bayan faduwar rana lokacin da
jan launi ya bar rabin Gabashin sama. Wasu mutane
basa iya azumi dan shekaru sun ja,
rashin lafiya, yanayin juna biyu, da sauransu, sai
a bada sadaka a maimakon, da/ko kuma
a maida azumin da aka sha daga baya.
Ko da yake asalin ruhin watan Ramadan ya kece kiyay
ewa daga wasu abubuwa 'yan
kadan kawai. Lokaci ne da za a dage da karfafa kwa
zo dan samun kamala a lamarin
neman kusanci ga Allah.
"Kuna jin kishi da yunwa
, ku ji shi ku yi rayuwa cikin shi, anan kuma yanzu
, ku kawo a
hankalinku tsananin wahala da kaifin kishi da yunwa
da zai kasance yanayin ranan a
Ranan tashin Kiyama.
Bada sadaka wa talakoki da marasa galihu.
Darajta iyaye da manya.
Yin kirki da nuna soyayya ga 'yayanka da yara.
Kula da nuna kaunaga 'yan uwa .
Kiyayayewa daga ba wa harce abun da bai kamata ba a
ko rada shi ba.
Kulle idonka daga abun day a kasance ba mutunci a k
ale shi.
Toshe kunnenka daga abun da zai kasance sabo mai ts
anani a ji shi.
Ka zama mai tausayi,hankali da kirki wa marayu sabo

da in ba ka nan, yaranka, in
da bukata, su ma za su kula daga wajen wasu.
Ka tuba zuwa ga Allah ka samu kusanci da shi.”
-
Annabin Tsira,tsarki ya tabbata a gare shi da iyali
n shi
Ban da yin azumi da kokarin hali na kwarai, Musulma
i suna bada lokacin su da karfin su
wajen sallah da addu’a zuwa ga Allah daya kadaitacc
e. Cikin wassu dararruka na
wannan watan, Musulmai za su kasance a farke dukkan
daren suna ibada.
Bayan rana na karshe na watan Ramadan, Musulmai sun
a bikin Eid ul Fitr dan su
karrama gama azumi. Su na taruwa dan sallah, cin a
binci, da kuma rarraba guzuri
daiden gwargwado (musamman ma yara). Ban da haka,
rana ne mai cike da jimami,
saboda watan Ramadana mai albarka da dukan dama da
yake badawa na tuba da lada ya
wuce sai wani shekara.
“Ina neman tsari da kirkin da Ka fi karkata ga, Ya
Ubangiji, kar karshen wannan
daren ya waye, ko watan Ramadana yazo karshe, kuma
na kasance ha ilau cikin
wanda aka kama cikin (ba a yafe ba) zunubi, wanda z
a a iya azabtarwa, a Ranar da za
a tsai da ni a gaban Ka.”
[Daga addu’ar ranar karshe na Ramadan, wanda Imam J
afar as-Sadiq,tsarki ya
tabbata a garish, ya koyar]
http://al-islam.org/faq

wanda ya cirato ya shigar Dan'uwa Sa'idu Funtua